**EPISODE 6**

**<u>CHARACTERS</u>**

*ALHAJI BATURE*

*HINDATU*

*MAI-UNGWA*

*INNA*

*LARABA*

*ASABE*

*JUMMAI*

**EPISODE 6, SCENE 1**

**OUTSIDE HAJIYA INNA'S COMPOUND – NORTHERN KADUNA.**

| | | |
|---|---|---|
| 1. | **MUSIC:** | **<u>THEME MUSIC</u>** |
| 2. | **SFX:** | **<u>LIGHT VEHICULAR MOVEMENT. HAWKERS SELLING THEIR WARES. BRISK FOOTSTEPS</u>** |
| 3. | **LARABA:** | **(COMING ON MIC)** Hajia Inna ina kwana? Ina fatan kin tashi lafiya |
| 4. | **HAJIYA INNA:** | Ina kwana Laraba, gaskiya ban ji dadi ba cikin dare, na yi ta fama da ciwon kai. |
| 5. | **LARABA:** | **(CONCERNED)** Ah, tun yaushe kika suma jin ciwon kan, Hajiya Inna? |
| 6. | **HAJIYA INNA:** | Ciwon kan fad a jifa jifa ne, amma yanzu kamar ya karu. Kamar kwayoyin maganin da nake amfani dasu basu aiki kuma. |
| 7. | **LARABA :** | Sanu Hajia Inna. Bara in duba ki in kuma auna jinin ki |
| 8. | **SFX:** | **<u>SOUND OF A BAG BEING UNZIPPED</u>** |

9. **HAJIYA INNA:** Na gode kwarai Laraba. Kina da kirki kuma kina kyautawa.

10. **SFX:** **PUMPING SOUND OF THE AIR BEING PUMPED IN THE BLOOD PRESSURE MACHINE BULB**

11. **LARABA:** Hajiya wannan kunburin na kafar ki kuma fa, tun yaushe kafar ta kunbura?

12. **HAJIYA INNA:** Satin da ta shige na gani fa, amma ban maid a hankali ba saboda baya min wani zafi.

13. **LARABA:** Hmm Hajiya, kamar jinin ki ya dan hau.

14. **HAJIYA INNA:** (**GETTING AGITATED)** Hawar Jini! Na mutu! **(TALKING TO SELF)** Inna, kin mutu, kin lalaci...

15. **LARABA:** **(CUTS IN, COMFORTING)** Aa Hajiyaa, don Allah bai kai haka ba, kada ki tasi han kalin ki.

16. **HAJIYA INNA:** (**UPSET)** Amma kin ci min ina da hawar jinni ba?

~~17.~~ **LARABA:** (**REASSURINGLY)** aa, Hajia Inna n ace miki jinin ki ya dan hau, chanji yanayin tsarin rayuwar ki zai iya magance hakan ma.

18. **HAJIYA INNA:** Kawai Laraba? Kina yi kamar abin ba babbar abu ne ba fa

19. **LARABA:** e, ba babbar abu bane idan baki tashi hankalin ki ba, kuma kika sauya abinda kike yauwan cin.

20. **HAJIYA INNA:** **(CURIOUS)** Karmar me zan daina ci.

21. **LARABA:** Ba masu yawa bani,Hajiya Inna. Zai taimaka indan kin rage cin nama, gishiri da kuma kitse.

22. **HAJIYA INNA:** **(SADLY)** Wai! Nefa ina son nama sosai.

23. **LARABA:** Za ki iya cid an kadan lokutalokuta, kina iya wa kuwa?

24. **HAJIYA INNA:** Dole zan iya ai, ina son in rayu in muri jikoki na ai.

25. **LARABA:** Yauwa, hakan yayi ai, zan kuma kawo miki maguguna daga asibitin idan ina dawowa da yamma.

26. **HAJIYA INNA:** Hmm, Laraba, na yi farin cikin dawuwar ki zama gidan nan, har na soma cin moreyar zaman ki, gashi inna samun kulla da lafiya ta a cikin gida na.

27. **LARABA:** (**LAUGHING)** Hajiya Inna, ki huta lafiya kuma ki kwartar da hankalin ki, na tafi asibitin, banda damin kanki ko?

~~28.~~ **HAJIYA INNA:** Nagode Laraba, zan yi yadda kika ce, allah bada saá

29. **MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**

**EPISODE 6, SCENE 2**

**Northern Kaduna – Alhaji Bature's Residence. Late Evening.**

30. **SFX:** **NIGHT NOISES. LIGHT VEHICULAR MOVEMENT. SOUND OF PLATES BEING COVERED.**

31. **HINDATU:** Alhaji Bature, ba ka ji dadin abincin bane? Ai kuma abincin da kakek so ne tuwon shikafa da miyar taushe ne.

32. **ALHAJI B:** Ki yi hakuri, abin kaunata Hindatu, labarin da nake son in gaya miki ne ke bata min rai.

33. **HINDATU:** Wace labara ce , Alhaji?

34. **ALHAJI B:** Ki kwashi kwanukan ki kai ki dawo muyi magana.

35. **SFX:** **SOUND OF PLATES BEING PACKED. BRISK STEPS. A SLIGHT PAUSE, STEPS COMING BACK ON MIC.**

36. **HINDATU:** **(SLIGHTLY BREATHLESS)** Alhaji, gani. Menene kake son ka fada min?

37. **ALHAJI B:** Matata Hindatu, ina son in sanar da ke cewar na sake samun wata matar dazan sake aura bada jimawa ba.

38. **HINDATU:** (**SURPRISED)** Amma Alhaji, baka jima da sakar dayar ba ai

39. **ALHAJI B:** **(IRRITATED)** Akwai takamamman tsawon lokacin d azan jira kafin in kara aure ne?

40. **HINDATU:** Alhaji, ne dai inna ganin yin hakan zai sa aga kamar kafiye sakin mata ne, kuma bayi da kyau.

41. **ALHAJI B:** Ni dai abinda mutane zasu fada ba zai shamin kai ba, abinda nasani shine na sake samun mata kuma zan aure tab a da jimawa ba.

~~42.~~ **HINDATU:** Amma da ka san za ka sake aure da sauri haka da baka ba Salamatu ko kuma daya daga cikin matan da ka sake dama ba?

43. **ALHAJI B:** **(FRUSTRATED)** Hindatu, kin san dai na auro su ne saboda Karin yaya. Kuma sun kasa daukar juna biyu Hindatu,

44. **HINDATU** Amma Alhaji, da ka sake hakuri dasu.....

45. **ALHAJI B:** **(ANNOYED)** Hindatu, yaya kike Magana kamar ba laifin ki bani yauwa aure das akin da ke yi.

46. **HINDATU:** **(SHOCKED)** Alhaji ne kuma?! Ta yaya?

47. **ALHAJI B:** Saboda kin kasa samar min da Karin yaya.

48. **HINDATU:** Amma Alhaji Bature, ba wai baka kada yaya bane, muna da yaya har uku tare da kai.

49. **ALHAJI B:** Hindatu, wa yannan yan mata ne!

50. **HINDATU:** **(UPSET)** Alhaji, Yan mata ba yaya bane?

51. **ALHAJI B:** E yaya ne, amma yara mata wata rana za suyi aure su tafi gidan mazajen su, tun da bamu dad a na miji wanene zai gaji sanaáta da nayi famar ginawa, kuma bayan raina wa zai kula da ke.

52. **HINDATU:** Alhaji, don Allah ka daina maganar mutuwa haka, baza ka mutu yanzu ba ai.

53. **ALHAJI:** Hindatu matata, ko ba jimawa ko ba dadewa tilas ne zan mutu wata rana, kuma jamaá zasu so su cin galimar kid a yayan ki mata, hakan da nake yi saboda ke ci fa.

54. **HINDATU:** Amma, duk sakesakin nan ba dole bane, jama'a sun soma magagannu ma.

55. **ALHAJI B:** **(CUTS IN, FIRMLY)** Hindatu, ni dai ina gaya miki ne tun da wuri, ki dai yi shirin kabar amarya.

56. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**EPISODE 6, SCENE 3**

**<u>NORTHERN KADUNA. HAJIYA INNA'S HOME.</u>**

57. **SFX:** **<u>NOISE OF CHILDREN PLAYING. POTS CLANGING.</u>**

58. **INNA:** **(CALLING OUT LOUDLY)** Asabe! **(PAUSE, LOUDER)** Asabe!! **(SHOUTING)** ASABE!!!

59. **ASABE:** **(OFF MIC, SHOUTS)** Naám, gani nan zuwa Hajiya (**BRISK STEPS) (ON MIC, SLIGHTLY OUT OF BREATH)** Gani nan Hajiya Inna.

60. **INNA:** **(ANGRY)** Asabe kina son ki bani wahala ne, me yasa kika kyalene ita kwala miki kira kafin ki amsa ni?

61. **ASABE:** Ah kiyi hakuri Hajiya, ban ji kiran bane.

62. **INNA:** Nars Laraba, na fada min kada in dinga sa kaina cikin tashin hankali har ma ihu ba daidai bane mani yanzu.

63. **ASABE:** **(IRRITATED)** Eh! Amma dai Inna na fada miki cewa ban jin kirar bane ai da sauri, abincin ki ya kusa ma.

64. **INNA:** Saboda da ma abincin ne na ke kwala miki kira, Nars Laraba tace min in rage cin gishiri da mai in kuma rage cin nama.

65. **ASABE:** **(ANGRY)** Wato, Labara na nufin muna baki guba anan hidan ko?

66. **INNA:** (**SNAPPING**) Wace irin Magana ne haka Asabe, Laraba ta bani sharawa akan in rage su ne saboda hawar jinin na.

67. **ASABE:** Hajiya Inna, Laraba fa Nars ce kawai, ki je ki ga likita da zai baki shawara daya fi.

68. **INNA:** Asabe, Laraba ai kwaririyar Nars ce, wanda tasan abinda ya kamata, kuma tana yin abinda ya kamata.

69. **ASABE:** **(UPSET)** Amma Hajiya, yaushe ta zo har tasan cewa abincin da muke baki ya fiye gishiri. Yaya ma aka yi ta sani? Ta taba cin girki na ne?

70. **INNA:** **(ANGRY)** Ya ishe ki haka Asabe! Haba! Kina son jin dadi na a zuciyarki kuwa?

71. **ASABE:** **(HURT)** Tabas mana, Hajia.

72. **INNA:** Toh, tun da haka ne, ki bi shawarar Laraba.

73. **ASABE:** **(RELUCTANT)** Idan shine abinda kike so Hajiya Inna, za mu rarrage abubuiwan daga abincin ki.

74. **MUSIC:** <u>**BRIDGE MUSIC**</u>

**EPISODE 6, SCENE 4**

<u>**NORTHERN KADUNA. ALHAJI BATURE'S RESIDENCE.**</u>

75. **SFX:** <u>**SOUND OF WEDDING PARTY. SOUND OF ULULATIONS.**</u> <u>**CHATTING AND MUSIC.**</u>

76. **BATURE:** **(HAPPILY)** Na gode Mai Unguwa, da ka hallarci wannan bikin.

77. **MAI UNGWA:** Alhaji Bature, ai dole ne in hallarci wannan daren auren

78. **BATURE:** Ina fatan Safiya zabi nagari ce.

79. **M/UNGWA:** Nima ina fatan, zaka yi hakuri da ita bana son ka saki ta kawai kamar yadda ka saki saurar hudu na chan baya

80. **BATURE:** Mai Unguwa, ni fa kokari nake in kare zuriyata, duk saurar sun kasa bani da namiji.

81. **M/UNGWA:** Bature, wannan bai kai hujar da zaka saki mata hudu a cikin yan shekaru biyu da suka wuce ba, ai yayi yawa.

82. **BATURE:** Yauwa, abinda nake cewa kenan Mai Unguwa, ina fatan Safiya ta Haifa min da namiji, nima in daina yawan auretaya.

83. **M/UNGWA:** Bature kana mance wa cewar yaya ko namiji ko ya mace, kyauta ne daga Allah.

84. **BATURE:** Na fahimta, amma duk wannar zafin nemar wa zai gada idan na mutu.

85. **M/UNGWA:** Bature kasan cewa kana daya daga cikin dattijan da matasa ke kallo anan alúmar tamu.

86. **BATURE:** Toh sai me idan suna kallo na?, nayi wani mumunar abu ne? Ne fa zuriya ta nake karewa.

87. **M/UNGWA:** **(FRUSTRATED)** Alhaji Bature, rashin hakurin ka wurin sakin matan ka, ba abu mai kyau bani, aure ibada ce, aure kuma na bukatar hakuri da tawakali.

88. **BATURE:** **(CHEERFULLY)** Ni bana son in ganka haka ranar aure na, na tabbata Safiya zata yi maganin dukan matsalar.

89. **M/UNGWA:** Tayaya zaka tabbatar?

90. **BATURE:** Ai, na dau lokaci na yi bincike kafin na zabo Safiya

91. **M/UNGWA:** **(CONFUSED)** Wane irin Bincike, yanzu ka zama kwarare ne wajen gano mata wanda ke iya haihuwa?

92. **BATURE:** Na farko dai, na gano cewa it ace kadai ya mace kuma tana da yanúwa maza da yawa, kuma a aurenta na baya tana da da namiji!

~~93.~~ **M/UNGWA:** Toh Bature, naga kayi lisafin ka, ina fatan lisafin tayi maka aiki.

94. **BATURE:** Ina fatan haka ni ma fa, ba wai ina jin dadin yawan aure da sake bane **(LAUGHS)** Kasan akwai tsada ai aure

95. **M/UNGWA:** Na yi maka murna da ka same abinda kake so matar da zata haifa maka dan namiji. Amma na baka shawarar ka kama kanka ko wato, mu hada kai tare don samar da hanyoyin tazarar haihuwa ko?

96. **BATURE:** **(AMUSED)** Mai Unguwa na dauki alkawarin yin amfani da hanyoyin tazarar haihuwa mudin na soma samun yaya, yayi?

97. **M/UNGWA:** Kuma ka daukan min alkawarin cewa kai da matar ka, za ku je asibiti domin neman sharawa kafin ku dau mataki.

98. **BATURE:** **(LAUGHS GREGARIOUSLY)** Ah, Mai Unguwa! Yana ji ka kuma zan yi amfani da shawarar ka.

99. **M/UNGWA:** Ina son in kuma gode maka da talafi da taimakon da kayi wa Husseini da na turo maka.

100. **BATURE:** Ai wancen ba matsala bane, nayi hakan ne saboda mune manya kuma ya dace mu tallafa mukuma taimaka ma matasan alúmar.

101. **M/UNGWA:** Toh bara in kyale ka saboda ka same lokaci da sauran bakin ka, amma kada ka mance da maganar da muka yi game da auren.

102. **BATURE:** **(UPBEAT)** Kada ka takura ma kanka Mai Unguwa, komai na tafiya dai dai. **(LAUGHS HEARTILY)**

103. **MUSIC:** **THEME MUSIC AND END CREDIT**